KHAMRU
UWAR LAIFI
Kullu muskirun Haraamun
Duk abu mai Bugarwa (sanya maye)
Haramun ne.
Bldr. Ibrahim Muhammad Ɗankyauri

ABUBUWAN DA KE CIKI.

1) Gabatarwa. 3
2) Kayan Maye. 4
2.1) Tarihin Samuwarsu. 4
3) Illolin kayan maye ga lafiyar jiki. 7
3.1) Illoli A Kimiyyance. 7
3.1.1) Illoli Ga Kwaƙwalwa. 7
3.1.2) Illoli Ga Gangar jiki. 8
3.1.3) Matsalar Taba Sigari. 9
3.1.4) Haɗa kayan maye fiye da ɗaya. 10
3.1.5) Haɗa kayan maye da Magani. 11
3.1.6) Kididdigar Kungiyar Lafiya. (WHO) 13
3.2) Illoli A Addinance 14
3.2.1) Khamru Uwar Laifi. 14
3.2.2) Kawar da Imani. 15
4) Hukuncin Musulunci Ga Kayan Maye. 16
4.1) Isra'i da Mi'iraji. 17
4.2) Kwaɗayin Khalifa Umar RA 18
4.3) Ayar Alƙur'ani ta Farko 19
4.4) Ayar Alƙur'ani ta Biyu 22
4.5) Ayar Alƙur'ani ta Uku 26
4.6) Ahadith (Hadisai) 27
4 7) Wasu Masu Son Zuciya 32
4.8) Hukuncin Wanda ya sha Kayan Maye. 32
5) Kammalawa. 34

1 GABATARWA

DA SUNAN ALLAH MAFI TAUSAYI MAFI JIN ƙAI

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin halittu. Wanda Ya haliccemu domin Ya jarrabamu. Wanda kuma Ya sanya Halal da Haram cikin abincin mu da abin shan mu. Tsira da Amincin Allah su daƈa tabbata ga Manzon Allah, Annabi Muhammad SAW tare da Sahabbansa Adalai da Matansa Tsarkaka da ragowar Al'ummar da ta yi riƙo da Sunnarsa har ya zuwa Ranar Sakamako.

Bayan haka, babban abinda yake damun al'umma a yanzu shine yawaitar kayan shaye-shaye masu sanya maye, ta yadda da yawa daga cikin matasan wannan zamani namu ke ta'ammali da su. Dalilin haka, yawan ta'addanci da rashin sanin ya kamata cikin al'umma ya ƙaru.

Sai naga dacewar rubuta wannan ƈan littafi domin nasiha ga waƈanda Iblis ya abkar cikin wannan hali da kuma jan hankali ga waƈanda ba su abka ciki ba, domin su ƙyamaci tare da gujewa wannan sha'ani na shaye-shayen kayan maye.

Da fatan Allah Ya amfanar da duk wanda zai sami damar karanta wannan littafi kuma Ya haƈa mu cikin ladan. Aamiiin.

2 KAYAN MAYE

Kayan maye sun ƙunshi abubuwa guda huɗu (4): - 1) Na farko kayan da ake sha tare da kwankwaɗa da baki kamar ruwa. Su ake kira burkutu ko giya (wannan suna Bahaushe ya ciro shine daga Kalmar “beer” da turanci), wadda ta kasu ita kuma kashi biyu - mai ƙarfi, kokino "whisky" da marar ƙarfi burkutun "wine" ko “beer” ,amma duk bugarwa suke yi. 2) Na biyu kayan da ake sha na hayaƙi kamar sigari shine ganye ko wiwi, wadda yake da sunaye masu tarin yawa: herbs, hemp, cannabis, marijiwana, hashish, da sauransu. 3) Na uku kayan da ake sheƙa a hanci ko ayi allurarsu, su ake kira hodar Iblis, sune opium, cocaine da heroin. Sauran sun haɗa da petrol, tiririn masai, penti. 4) Na hudu kayan da ake yin shayi ko kunun zaƙi da su. Amma wannan a fitinar gargajiya, sune zaƙami da wiwi.

Taba da anguru, ba sa cikin kayan maye saidai amfani da su na lalata jiki ya haifar da rashin lafiya mai tsanani da kuma mutuwa da wuri.

2.2 TARIHIN SAMUWAR KAYAN MAYE.

Kayan maye sun daɗe da samuwa cikin tarihin bani Adama. Duk wanda zai faɗi lokaci ƙaiyadadde ba shi da tabbas. Amma dai tun kafin zuwan Musulunci, Labarabawa an sansu da kwankwaɗar khamru. Da Musulunci ya zo sai ya ɗora su kan Gwadabe mafi inganci domin kare musu hankali da tunani wanda zai kai su ga

bunƙasar ci gaban rayuwa da ilimin abubuwan dake kewaye da ɗan Adam. Wannan kuwa lallai a zahiri yake ta yadda duk wani tushen ci gaba na ilimin fasaha da kimiyya, asalinsa ƙasar Musulmai ne ko kuma Musulmi ya bayar da wata ƙwaƙƙwarar gudummawa ciki. Misali na baya-bayan nan shine samar da lantarkin SOLAR wadda yake amfani ba tsayawa cikin na'urorin da aka harba cikin sararin Subuhana masu tura saƙonni duk wani ɓangare na duniya, da kuma na'urorin da aka harba kan wasu duniyoyin domin bincike da nazari, to tushensa Musulmi ne mai suna, Hassan Kamel Al-Sabbah ɗan asalin Lebanon (Injiniyan Lantarki da ƙirƙire-ƙirƙire 1894-1935), ya rasu yana ɗan shekara arba'in cikin hatsarin mota a America. Wannan kenan.

A ƙasashen da ba na Musulmai ba, suna iƙrarin fara samuwar giya tun lokacin ƙarni na 13,000 kafin Annabi Isa AS. An sami tarihin samuwar giya a ƙasar Sin (China) ta arewa tsakanin shekara ta 7,000 zuwa 6,500 kafin Annabi Isa AS.

Anan ƙasar Hausa giya tana samuwa ne cikin Hausawa Maguzawa, waɗanda ba su Musulunta ba har yanzu. Suna yin giya ne ta hanyar tsuma gero ko dawa har sai ya fara tsiro sannan su markaɗa sai su dafa. Shike nan burkutu ta samu. Yawanci sukan sha ta daidai Misali, idan za su yi aikin ƙarfi kamar noma da huɗa, domin samun ƙarfi da kuzari. Idan yamma ta yi an gama aikin ƙarfi sai kuma a zauna zaman kwankwaɗarta har su bugu.

Amma lokacin da hatsin yayi tsiro, da sun baza shi ya bushe raƙaƙau, idan sun niƙa ya zama gari, kuma suka yi kunun zaƙi ko koko, to ba zai bugar ba, sai dai kawai ƙarin kuzari da nishaɗi. Wannan shi ake kira Maltina, ko Maltex.

Haka waɗansu ƙabilun kamar na Larabawa a da can, su kuma inabi ko dabino suke tsumawa kwana da kwanaki har ya zama giya idan ya tsumu sosai. Shi ya sanya a lokacin Manzon Allah SAW ya hana tsuma duk wani tsimi sama da kwana uku. Domin idan ya wuce kwana uku, zai yi "fermentation" ya koma giya.

A yanzu giya haramun ce ga Musulmi, amma wasu na yin wata dabara ta tsuma furar gero har ta yi tsami. Wannan wani salo ne na yin giya a fakaice, domin kana shan ta da yawa, buguwa za ka yi. Allah Ya sauwaƙe.

Ƙabilu daban daban tun da can, sukan yi amfani da wani nau'i na giya domin bukin murnar wani abin al'ada kamar aure, rasuwa, ko kuma wajen al'ada ta bautawa abinda da suke bautawa.

Sukan sha giya ne domin samun nishaɗi na wani ƙanƙanin lokaci, daga nan kuma sai su shiga ruɗun bugawa ta yadda wasun su suke ammai, kashi a kwance, ko jefa rayuwarsu cikin hatsarin rasa rai ko jin mummunan ciwo. Da yawa sukan sha giya ko wani abin maye domin aikata mummunan abu cikin al'umma, kamar faɗe, sata, kisan kai na waninsa ko kansa.

Amma da can, da yanzu, wasu sojojin da ba Musulmai ba suna shan giya ne ko wani "substance" domin kawar musu da tsoro a filin yaƙi, kamar yadda suke kiranta "Ruwan Kawar da Tsoro" (da rashin tausayi). Kuma haka abin yake a zahiri har yanzu. Ta yadda duk wani nau'i na zalunci da wasu ke yi ga wasu, sai sun sha sun yi mankas, suke iya aiwatarwa. Kwanan nan Sheikh Ahmad Gumi na ji yana cewa (bayan ya dawo daga tattaunawa da Fulani yan fashin daji), "Yara ƙanana cikinsu yan fashin dajin, ba abinda ake ba su sai wiwi da ragowar "substance" domin kawar musu da imani da tausayi ta yadda za su keta haddin Allah ba tare da ko jin ɗar ba. Shi yasa duk wani mai ta'ammali da kayan maye zaka ga ba shi da ta ido, ba ya tsoro, kuma zuciyarsa a ƙeƙashe take ko akan mahaifansa ne kuwa.

3 ILLOLIN KAYAN MAYE GA JIKIN ƊAN ADAM

3.1 ILLOLI A KIMIYYANCE:

3.1.1 ILLOLI GA ƘWAƘWALWA.

Duk wani kayan maye yana taɓa ƙwaƙwalwar wanda ya sha su ne. A kimiyyance, sinadarin "Ethenol" ne a cikin giya ta ruwa da aka sani. Ƙarfin ta ya dangana ga yawan Ethenol cikinta. Shi wannan sinadari yana bin hanyoyin jini ya kai ga sassan jikin ɗan Adam har ƙwaƙwalwa, ta yadda yake rikitar da mai ita cikin tunaninsa na

ɗabi'a. Sai tunanin sa da yake gani da fahimtar abubuwa su sauya daga abinda aka sani na daidai zuwa abinda ba a sani ba watau sharri.

Idan wannan sinadari ya fara yawa cikin jinin mutum to zai yi wahala ya daina shan giya.

Bincike ya nuna cewar giya tana sanya hauka na ɗan wani lokaci. Daga baya mutum ya dawo daidai cikin hankalinsa idan ta sake shi. Amma ragowar kayan maye irinsu wiwi, heroin, cocaine da sauransu, sukan sanya hauka ne da kaɗan da kaɗan wadda ba a warkewa idan ya kai wani mataki.

Banda wannan sinadari na "Ethenol" da ke cikin giyar da aka sani, akwai waɗansu sinadaran cikin wasu kayan mayen na giyar ruwa waɗanda hatsarinsu ga ƙwaƙwalwa ya ninninka na "Ethenol". Sune kamar su, "isomethyl", "isopropanol", "isobutanol" da sauransu.

3.1.2 ILLOLI GA GANGAR JIKI (CIKI DA WAJE).

Kamar yadda ya gabata, cewar sinadarin "Ethenol" ne ke gudana cikin jinin ɗan giya ko ƴar giya, ta yadda yake kaiwa ga duk wata ƙanƙanuwar halitta (cell) a cikin jikin ɗan Adam. Idan ya kai ga inda ya kai, sai ya fara canza halittar wannan gaɓa ko na'ura da take yiwa ɗan Adam aiki a cikin jikinsa ba tare da ya sani ba. Idan ethenol yayi yawa a cikin jini, yakan taɓa hanta, saifa, ƙoda, zuciya da

azzakari (wutsiya) ta yadda zai hana ta gyaɗa kai. Mace balagaggiya mai ta'ammali da kayan maye, suna shafar mahaifarta (womb) ta yadda idan ta ɗauki ciki, abinda ta samu zai iya zama mai tauyayyiyar halitta tun yana ciki. Sannan duk waɗannan na'urorin na jikin ɗan Adam, watau hanta, ƙoda, saifa, azzakari, mahaifa da sauransu, na iya kamuwa da ciwon sankara ko daji (cancer). Kai har jinin zai iya samun ciwon (cancer). Allah Ya sauwaƙe.

3.1.3 MATSALAR TABA.

Ita "ordinary" taba sigari bata bugarwa, sai dai a kimiyyance, illar da kayan maye ke yiwa ɗan Adam a jiki, to taba tafi su illa ga jikin ɗan Adam. Haɗi da wannan ga almubazzarancin ƙona dukiya (kuɗin da ake sayan tabar). Shi ya sanya ƙungiyar duniya ta lafiya ta shar'anta rubuta gargaɗi ga kowanne kwalin Taba cewar "Kana cikin hatsarin rasa rayuwarka da wuri idan kana shan Taba". Da wannan malaman Musulunci a wannan zamanin suka haɗu (ijma'i) kan Haramcin shan karan sigari da shan lope. Domin Allah Ya ce a cikin Alƙur'ani mai Tsarki ".....Kada ku jefa kawukanku ga halaka...." Surah Al-Baƙara aya ta 195.

3.1.4 HAƊA KAYAN MAYE BIYU KO UKU KO FIYE DA HAKA A LOKACI GUDA.

Wasu mashayan, sukan haɗa kayan maye fiye da nau'i ɗaya a lokaci guda su yi ta sha. To wannan kuma yafi komai hatsari, domin kowanne akwai irin illar da yake yi a jikin ɗan Adam. Idan mutum yana son ya haukace da wuri, ko yana son ya baƙunci lahira cikin sani, to ga hanya nan mafi sauƙi. Allah ya kiyaye.

MISALAI

Haɗa Giya da hodar Iblis (Cocaine) - Coca Wine

Abinda wannan zai haifar cikin jini da ƙwaƙwalwar wanda ya sha su a lokaci guda shine sinadarin "cocaethylene". Shi wannan sinadari yana da matuƙar hatsari ga zuciya wadda zai iya sanyawa ta buga fiye da kima ko ƙasa da kima "Hypertension ko Hypotension" har ta daina aiki - mutuwa kenan.

Haɗa Giya da Wiwi (Cannabis) - Canna Wine

Abinda da wannan zai haifar cikin jini da ƙwaƙwalwar wanda ya sha su a lokaci guda shine ƙarin yawan shigar sinadarin "tetrahydrocannabinol" cikin ƙwayoyin halittar jini da ƙwaƙwalwa wadda sakamakon hakan shine, saurin raunatasu tare da kashe su - hauka kenan, sannan mutuwa. Ta ko ina ba sauƙi.

3.1.5 HAƊA KAYAN MAYE DA MAGANIN ASIBITI NA HALAL A LOKACI GUDA.

Wasu mashayan, sukan haɗa giya da maganin asibiti na wata sananniyar cuta a lokaci ɗaya. Wannan yana haifar da wasu matsaloli ɗoriya kan cutar da aka sha maganin domin ta.

MISALAI

Haɗa Giya da Metronidazole (maganin zawayi)

Metronidazole magani ne dake kashe ƙwayar cutar zawayi mai suna "Clostridioides difficile bacteria". Bincike a da ya nuna cewar haɗa wannan magani tare da giya a lokaci guda na haifar da canjin yanayin sinadaran dake cikin tumbin marar lafiyar dake fama da zawayi, sai su haifarmasa da ƙarin wata matsalar ta daban ɗoriya kan zawayi.

Haɗa Giya da Aspirin (ko wani maganin hana damuwa).

Suma irin waɗannan magungunan, tare da waɗanda suke hana ciwon jiki irin su diclofenac, epadrine, codine, idan an sha su tare da giya, yanayin iskar gas dake cikin tumbin wanda ya sha su, takan canza ta haifar da tsatstsafar jini cikin tumbi "gastrointestinal bleeding" tare da haifar da amosanin tumbin "peptic ulcers".

Haɗa Giya da Caffeine (Sinadarin dake cikin Coffee da Goro)

Shan maganin dake ɗauke da sinadarin Caffeine (Cafenol) ko lemon gwangwani na "energy drinks", tare da giya na haifar da ƙarin son shan giyar na fitar hankali. Wannan zai haifarwa da mutum kullum ya zama cikin giya kamar mota. Mun kuma karanta yadda giya take lalata sassan ɗan Adam.

Haɗa Giya da Nicotine (Sidarin dake cikin Taba Sigari)

Shima wannan sinadarin ana sanya shi cikin lemon kwalabar wasu ƙasashen da nufin wartsakarwa. Amma ana haɗa shi da giya to shima abinda Caffeine ya haifar shi yake haifarwa. Ƙari kan wannan, nicotine dake cikin sigari na dagargaza huhu.

3.1.6 ƙIDIDDIGAR ƙUNGIYAR LAFIYA TA DUNIYA (WORLD HEALTH ORGANIZATION) "WHO" KAN CUTUTTUKA DA MACE-MACE SAKAMAKON KAYAN MAYE.

"WHO" ta ce, mace-mace da ake samu a duniya duk shekara, kimanin miliyan biyu da dubu ɗari shida (2,600,000) shaye-shayen kayan maye ne yake haifar da su. ƙari kan wannan ta ce, amfani da kayan maye ya haifar da matsalolin lafiya cikin kaso 4.7% na al'ummar duniya.

A cikin wannan yawa na marassa lafiya, waɗanda ke amfani da miyagun kayan maye sun kai kaso 6.9% na maza, sannan kaso 2.0% mata ne. Kayan maye ne mafi hatsarin haddasa mutuwar matasa a yau a duniya waɗanda shekarunsu ya kama daga 20 zuwa 39. Wannan tsakani na shekaru, na da mace-mace na mutane har kaso 13%. Kuma al'ummar da tafi taɓuwa sune waɗanda basu ci gaba ba cikin rayuwa da ƙasashe matalauta.

Sannan wani binciken ya nuna cewar a duk duniya, ƙasashen Musulmai ne suka fi ƙarancin masu matsalar shan kayan maye, domin shan su a Musulunci Haramun ne.

Wannan tasa makircin ƙasashen duniya ya haifar da cewa a samar da miyagun kayan maye a cikin al'ummar da ba Musulmai ba, domin kaiwa al'ummar Musulmai ta yadda za a daɗa lalata Tarbiyyar su. Za ka iya fahimtar haka a nan Nijeriya, ta yadda duk miyagun kayan mayen da ake samu anan Arewa daga ƙasar Kudu ake kai musu, musamman daga ƙasar Inyamurai.

Saboda haka, ƙara tabbatar da SHARI'AR MUSULUNCI a Arewa WAJIBI ne tare da bata KARIYA ta Musamman.

3.2 ILLOLI A ADDINANCE;

3.2.1 A ADDININ MUSULUNCI, "KHAMRU" GIYA (DA DUK WANI KAYAN MAYE) ITA CE UWAR LAIFI.

Hadith daga Sunan An-Nasa'i v6 Babi na 44: Zunuban da Shan Kayan Maye yake haifarwa, kamar Barin Sallah, Kisan Kai da Aikata Zina.

5669. An hakaito daga Abu Bakar bin 'Abdur-Rahman bin Harith cewa babansa ya ce, "Na ji Uthman RA ya ce: 'Ku guji "Khamr", (kayan maye irin) giya, domin giya ita ce uwar duk wani laifi. Anyi wani mutum cikin wata al'umma da ta gabace ku mai yawan 'ibada. Sai wata matar banza ta ji kawai shi take so (yayi fasiƙanci da ita).

Sai ta aika gareshi da wata yarinyarta baiwa, cewa ya zo domin ya bayar da shaida kan wani abu. Saboda haka sai mutumin ya ɗauki hanya tare da yarinya baiwa zuwa ga wannan matar banza.

Har suka kai ga gidanta inda duk lokacin da suka shiga ta wata ƙofa sai ta kulle ta a bayansu, har ya isa ga wata tsaleliyar mace, wadda take da wani yaro da kuma wani mazubin giya.

Sai (matar banzan nan) ta ce, "Na rantse da Allah ban kirayeka don shaidar wani abu ba, kawai so nake yi, ka yi zina da Ni, ko ka kashe yaron nan ko ka sha giyar nan.

(Matar banza kirarinta a Hausa shine: (Nakiyar kan juji, ga kyau ga zaƙi, sai dai kash tana cikin ƙazanta), ko kuma (juji baka ƙyamar shara) ko kuma (‘yar gagara baƙar ashana ƙona gari)).

(Sai ya ga cewar ai shan giyar yafi sauƙi akan ya aikata zina ko ya yi kisan kai).

(Saboda haka), sai ya ce ba Ni kofi, ya karɓi giyar ya sha. Ya ce ƙaro. Kai tana ba shi giya (har sai da ya ƙwale, ya bugu) sannan ya aikata zinar da ita, kuma a lokaci guda ya kashe yaron.

Saboda haka, ku guji giya, Na rantse da Allah, Imani tare da kwankwaɗar giya ba sa haɗuwa guri ɗaya, domin dole wani a cikin su ya kori wani". Sahih. Ƙarin bayani cikin baka daga gareni ne.

3.2.2 IMANIN MAI SHAN GIYA YANA BARINSA LOKACIN DA ZAI SHA GIYAR DA KUMA LOKACIN DA YAKE SHAN TA.

Hadith daga Littafin Sahih Muslim

[208] 104 - (.....) An karɓo daga Abu Huraira cewar Manzon Allah SAW ya ce, "Ba wani mazinaci, da yake kasancewa mumini lokacin da yake zina, ba wani ɓarawo, da yake kasancewa mumini lokacin da yake sata, ba wani mashayin kayan maye, da yake kasancewa mumini lokacin da yake shan kayan maye (ƙwalewa); amma za a iya karɓar tubansa bayan haka".

IMANI shine gaskatawarka ga ALLAH, MANZONSA DA MUSULUNCI. Wannan yana nuni ga cewa, Imani na raguwa da aikin saɓo, haka aikin ɗa'a yana ƙara Imani. Saboda haka, babbar illar shan giya a Addini shi ne raba mutum da Imaninsa. Allah Ya kiyayemu.

Sannan karɓar TUBA ya ta'allaƙa ne da abubuwa ko sharuɗa guda huɗu zuwa biyar, kamar yadda mai ahallari ya faɗa: 1) Ciruwa ko barin aikata wannan saɓon lokacin da ake cikin yinsa. 2) Nadamar abin da ya gabata na saɓon. 3) Tuba da neman Gafarar Allah. 4) Yin alƙawarin ba za a sake aikata wannan saɓo ba. 5) Mayarwa da mai hakki, hakkinsa idan ya shafi dukiyar wani, ko neman yafiyar wani idan ya danganci keta mutuncin wanin. Sai cikon na shida wadda mai ahallari bai kawo ba: 6) Tuba kafin gargarar Mutuwa ta abkawa mutum.

4 HUKUNCIN MUSULUNCI GA KAYAN MAYE

Ƙa'ida ta Usul Fiqhu shine, babu wani abu da Allah SWT zai haramta mana, ko ManzonSa face akwai wani sharri tattare da shi ga al'umma ɗaiɗaikunsu ko jama'arsu gaba ɗaya a dunƙule. Haka babu wani abu da Allah AWJ zai halasta ko ManzonSa face abu ne mai alkhairi ga al'umma ɗaiɗaikunsu ko jama'arsu gaba ɗaya a dunƙule. Kuma duk abinda aka haramta a Musulunci, to an musanya shi da wani abin mafi inganci. Wannan ita ce SHARI'AR

MUSULUNCI wadda kafirai da kuma munafukan Musulmai ke ƙyamata.

Kafin saukar da Haramcin giya da sauran kayan maye, Larabawa Musulmansu da Kafiransu duk shan ta suke yi. Kuma dai mu sani cewar sunan giya da Larabci shine "Khamr". Wannan suna ya haɗa da duk wani abu mai jirkita tunani har yasa mutum ya ƙwale watau ya bugu ya fita daga haiyacinsa na daidai ya koma mai yin tamɓele da hauka da rashin mutunci idan ya ɗirketa da yawa. Duk da cewar, Haramcin shan giya bai baiyana ba farkon Musulunci, da yawan Musulmai suna taka tsan-tsan da ta'ammali da ita, tun kafin a haramta musu. Wannan kuwa ya dace da Hadisin Israa'i da Mi'iraaji kamar haka:

4.1 ISRA'I DA MI'IRAAJI

Daga littafin Bukhari V4.

3394. An rubuto daga Abu Hurairah RA ya ce, Manzon Allah SAW ya ce, "A rãnar Isra'ina, (tafiyar dare zuwa Israel da Saman Bakwai), Na ga Annabi Musa AS wanda yake siriri ne mai kanannaɗaɗɗiyar suma, mai kama da wani daga ƙabilar Shanu'a. Na ga Annabi Isa mai matsakaicin tsaho da jar fuska kamar ya fito daga wanka. Kuma Na yi kama da Annabi Ibrahim fiye da kowannen mutum daga tsatsonsa. Sai aka bijiro mini da kofuna guda biyu, guda cike da Madara, guda cike da giya. Mala'ika Jibril ya ce, "Sha duk wanda

kake so". Sai na ɗauki kofin Ɱadara Na sha. Mala'ika Jibril ya ce "Ka dace da fitrah (Addinin Gaskiya watau Islam), da ka ɗauki giyar, al'ummar ka sai ta ɓace (ga hanya madaidaiciya)".

Tun daga kan wannan Hadisi, za mu fahimci shan kayan maye ɓata ne, kuma Haramta su shine mafi dacewa cikin al'umma.

4.2 KWAƉAYIN KHALIFA UMAR (R.A.) BAYAN SAUKAR DA HARAMCIN KAYAN MAYE.

Hadisi daga littafin Abu Dawud v4 kan Haramta giya, da kwaɗayin Umar RA ga samun bayanan wasu hukunce-hukunce, kafin wafatin Manzon Allah SAW.

3669. An rubuto daga Ash-Sha'b RA, daga Ibn 'Umar, daga 'Umar (babansa) ya ce: "Ranar da aka saukar da Haramcin giya, ana yin ta ne da abubuwa guda biyar: inabi, dabino, zuma, alkama da sha'ir. 'Khamr' shine duk abinda ya lulluɓe hankali. Akwai abubuwa uku da na yi kwaɗayin Manzon Allah SAW ya yi mana bayaninsu kafin barin mu - hukunci game da gadon (inheritance) kaka (grandfather), Al-kalalah, da wasu nau'i na Riba". Sahih.

4.3 AYA TA FARKO CIKIN HARAMTA KAYAN MAYE:

Allah SWT Ya ce:

يَسۡـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلۡخَمۡرِ وَٱلۡمَيۡسِرِۖ قُلۡ فِيهِمَآ إِثۡمٞ كَبِيرٞ وَمَنَٰفِعُ لِلنَّاسِ وَإِثۡمُهُمَآ أَكۡبَرُ مِن نَّفۡعِهِمَاۗ وَيَسۡـَٔلُونَكَ مَاذَا يُنفِقُونَۖ قُلِ ٱلۡعَفۡوَۗ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلۡأٓيَٰتِ لَعَلَّكُمۡ تَتَفَكَّرُونَ

Suna tambayar ka game da giya da cãcã. Ka ce: "A cikinsu akwai zunubi mai girma da wasu amfãnõni ga mutãne, kuma zunubinsu ne mafi girma daga amfaninsu." Kuma suna tambayar ka mẽne ne zã su ciyar; ka ce: "Abin da yayi ragowa." Kamar wancan ne Allah Yake bayyanawar ãyõyi a gare ku; tsammãninku, kuna tunãni. [Surah Al-Baqarah: 219]

ASBABUN NUZUL (Sababin Saukar aya) na Imam Al-Waahidi ya ce:

Wannan aya ta sauka ne dalilin Umar bin Khaɗɗab da Mu'azu bin Jabal da kuma wasu taron Lansarawa waɗanda suka jewa Manzon Allah SAW suna masu neman ya basu fatawa kan Hukuncin "Giya da Caca, domin su biyun suna tafiyar da Hankali da kuma Dukiya". Sai Allah Ya saukar da wannan aya.

TAFSIRIN ƘURƊABI.

Ga kaɗan daga Imam Ƙurɗabi cikin Tafsirinsa ga wannan aya:

Ya ce "akwai mas'aloli kamar guda tara cikin wannan aya". Amma zamu taƙaita kan uku kawai waɗanda suka shafi abinda muke magana kai tsaye.

Mas’ala Ta farko,

Faɗin "Suna tambayarka", masu tambaya anan sune Muminai kamar yadda ya gabata (cikin Asbabun Nuzul). Kalmar "Al-khamru" kuwa an cirota ne daga "khamara" ai "satara" sitirtawa ko rufewa ko ɓoyewa ko lulluɓewa ko kawarwa. Kamar yadda yazo cikin faɗinka "Khimarul Mar'ati", abin lulluɓe fuskar mace, (niƙabi). Duk abinda ya rufe wani abu to yayi "khamarahu". Shine ne ma faɗin Hadith "Khammiruu Aaniyatakum", "Ku rurrufe tukwananku (mazuban ruwanku)". Ta yadda giya take ɓoye, rufe, sitirta hankali ta gusar da shi shi ya sanya aka bata sunan Al-Khamru da Larabci.

Mas’ala Ta biyu,

Jumhurun al'umma sun tafi akan cewar duk abu mai yawan da ya sanya maye, daga giyar inabi ne ko giyar waninsa, to HARAMUN ne kaɗan ɗinsa ko da yawansa. Maganganu akan cewar wai giyar da akayi da inabi (ko dabino) sune kawai Haramun kuskure ne, hadisai ne dha'ifai. (ƙabilun Larabawa suna da wadatar Inabi da dabino ne, kuma daga garesu suka san yadda za suyi giya a lokacin. Wasu ƙabilun ba su da wadatar waɗancan ɣaɣan itacen, sai wani abin daban. Kamar Maguzawan Hausawa waɗanda suke yin giya

da hatsi kawai). Saboda haka, duk abu mai bugarwa irin yadda giyar inabi ko giyar dabino take bugarwa, to duk hukuncinsu ɗaya - HARAMUN ne. ("Kullu muskirun HARAMUN", Hadith).

Mas'ala Ta uku

Waɗansu daga cikin masu Tafsirin Alƙur'ani sun ce babu wani abin karramawa ko nagarta da Alllah zai yi kira gareshi face sai Ya baiwa wannan Al'umma. Yana daga cikin karamci da ihsaninSa ga wannan al'umma ta yadda bai saukar da Shari'a gaba ɗayanta a lokaci ɗaya ba, sai kaɗan kaɗan cikin lokaci mai tsawo. Wannan ita ce ayar farko mai nuni zuwa ga haramcin giya. Daga nan sai "La taƙrabus salaata...." Sai kuma "Innamaa yuridukumush Shaiɗan.....". Ƙarshen rubutowa daga Tafsirin Imam Ƙurɗabi. Maganar da ta zo cikin baka, ƙarin bayanina ne kawai.

Idan hankali ya gushe me ke faruwa? Tamɓele da hauka da rashin mutunci kawai.

Kun ga irin gaskiyar Sahabban Manzon Allah SAW da irin son riƙon su ga Addini. Sun sani cewar lallai akwai tarin sharri mai yawa cikin waɗannan abubuwan - Giya da Caca, shi yasa suka fara ƙyamatar su. To ba su tsaya nan ba, sai da suka dangana ga Annabi SAW domin faiyace musu hukuncinsu. Tun jahiliyya suke shan ƴar abarsu, kenan abu ne wanda ya zama ɗabi'arsu. Daina shi faraɗɗaya zai yi musu wahala ƙwarai. Shine dalilin da ya sa aka bisu sannu a hankali har zuwa ayar ƙarshen da ta haramta kwata-kwata.

4.4 AYA TA BIYU CIKIN HARAMTA KAYAN MAYE:

Allah SWT Ya ce:

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقۡرَبُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَأَنتُمۡ سُكَٰرَىٰ حَتَّىٰ تَعۡلَمُواْ مَا تَقُولُونَ وَلَا جُنُبًا إِلَّا عَابِرِي سَبِيلٍ حَتَّىٰ تَغۡتَسِلُواْۚ وَإِن كُنتُم مَّرۡضَىٰٓ أَوۡ عَلَىٰ سَفَرٍ أَوۡ جَآءَ أَحَدٞ مِّنكُم مِّنَ ٱلۡغَآئِطِ أَوۡ لَٰمَسۡتُمُ ٱلنِّسَآءَ فَلَمۡ تَجِدُواْ مَآءٗ فَتَيَمَّمُواْ صَعِيدٗا طَيِّبٗا فَٱمۡسَحُواْ بِوُجُوهِكُمۡ وَأَيۡدِيكُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَفُوًّا غَفُورًا

Yã ku waɗanda suka yi ĩmãni! Kada ku kusanci salla alhãli kuwa kuna mãsu mãye*, sai kun san abin da kuke faɗa kuma haka idan kuna mãsu janaba, fãce mai ƙẽtare hanya, har ku yi wanka. Kuma idan kun kasance majinyata, ko kuwa a kan tafiya ko kuwa wani daga cikinku, idan ya zo daga kãshi, kõ kuwa kun shãfi mãtã ba ku sãmi ruwa ba, to ku nufi, fuskar ƙasa mai kyau, ku yi shãfa ga fuskokinku da hannuwanku (taimama). Lalle ne Allah Yã kasance Mai yãfẽwa Mai gãfara. [Surah An-Nisāʾ: 43]

ASBABUN NUZUUL

Asbabun Nuzuul (Sababin Saukar aya) na Imam Al-Waahidi ya ce:

Faɗin Allah 'Azza wa Jalla "Ya ku waɗanda kuka yi Imani! kada ku kusanci sallah alhali kuwa kuna masu maye". An saukar da ita dalilin wasu daga cikin Sahabban Manzon Allah SAW, sun kasance suna shan giya sai su halarci sallah suna cikin maye, har su kasa fahimtar raka'a nawa suka sallata tare da rashin sanin abinda suke furtawa

cikin sallar. (Sai ya kawo hadisi wadda zan taƙaita cikin sanadinsa). An karƀo daga 'Aliyu bin abu Ɗaalib ya ce: 'Abdurrahman bin Auf ya yi abinci a gidansa sai ya gayyato wasu daga cikin Sahabban Manzon Allah SAW, sai suka ci suka sha (har da ƴar giyar da aka saba sha), har zuwa magariba. Sai suka gabatar da ɗayansu domin jagorancin yi musu salla (ta magariba). Sai ya karanta musu "Kul Ya aiyuhal Kaafiruun" (bayan fatiha). Amma ya kasa kawo ta daidai, (saboda uwar laifi ta tafi da wani ƀangare na hankalinsa). Shine Allah Ya saukar da "Ya aiyuhal Mu'minuna la taƙrabus salata wa antum sukaaraa".

TAFSIRIN QURƊABI

Ga kaɗan daga Imam Ƙurɗabi cikin Tafsirinsa ga wannan aya:

Ya ce, "A cikin wannan aya akwai mas'aloli guda arba'in da huɗu". (Saboda haka idan zamu kawo su anan, to wani sabon littafin za mu rubuta, dalilin haka, zamu taƙaita ne kan abinda ya shafi ƀangaren farko na ayar watau "Ya ku waɗanda... har zuwa kuna masu maye").

Faɗinsa Ta'ala "Yã ku waɗanda suka yi ĩmãni! Kada ku kusanci salla alhãli kuwa kuna mãsu mãye" Allah SWT Ya keƀance Muminai cikin wannan maganar saboda sune kawai suke tsayar da sallah bayan shan giya har ƙwaƙwalensu su sami rikici. (Duk da a ƙwale suke, Allah SWT kiransu yayi da sunan Muminai). Su kuwa kafirai ba sa sallah ko sun sha giya ko basu sha ba. Abu Dawud ya rubuto

daga Umar bin Khaɗɗabi RA cewa, lokacin da aka saukar da haramcin giya sai (Umar) ya ce "Ya Allah baiyana mana wani bayani gamshashshe cikin (al'amarin) giya". Sai ayar da take cikin Baƙara ta sauka "Suna tambayarka game da giya da caca". Ya ce, sai aka kira Umar aka karanta masa wannan ayar. (Har yanzu dai Umar bai gamsu ba) Sai ya ce "Ya Allah baiyana mana wani bayani gamshashshe cikin (al'amarin) giya". Sai ayar cikin Nisaa'i ta sauka, "Yã ku waɗanda suka yi ĩmãni! Kada ku kusanci salla alhãli kuwa kuna mãsu mãye". Mai kiran sallar Manzon Allah yakan ce duk lokacin da aka tsayar da sallah "Ku saurara, kada daɗai ku kusanci sallah kuna maye". Sai aka kira Umar aka karanta masa wannan ayar. (Har yanzu Umar RA yana cikin damuwa), sai yace "Ya Allah baiyana mana wani bayani gamshashshe cikin (al'amarin) giya". Sai wannan ayar ta sauka "Fahal antum muntahuun?", "Shin zaku hanu?". Sai Umar yace "Intahainaa", "Mun hanu".

Kuma Sa'id bin Jubair ya ce, mutane suna kan ɗabi'arsu ta jahiliyya har zuwa lokacin da aka umarce su ko aka hanasu. Sun kasance suna shan (giya) farkon Musulunci har zuwa saukar "Suna tambayarka game da giya da caca". Suka ce zamu sha ta domin amfani, amma ba domin aikata saɓo ba. Sai wani mutum ya sha sannan ya wuce gaba domin limancin Sallah. Sai ya karanta musu "Kul ya aiyuhal kafiruun! A'abudu ma ta'abuduun" (maimakon 'ʞul ya aiyuhal kafiruun! Laa A'abudu ma ta'abuduun'), sai wannan aya ta sauka "Yã ku waɗanda suka yi ĩmãni! Kada ku kusanci salla alhãli kuwa kuna mãsu mãye". Sai suka ce, (shike nan za mu sha) amma

ba dab da Sallah ba. Sai Umar ya ce "Ya Allah baiyana mana wani bayani gamshashshe cikin (al'amarin) giya". Dalilin haka wannan ayar ta sauka (ta ƙarshe cikin haramcin shan giya): "Innamaa yuridush Shaiɗanu....." har zuwa ƙarshe. Sai Umar ya ce "mun bari", "mun bari" (watau shan giyar). Daga nan mai kiran sallar Manzo ya shiga gari yana yekuwa cewar "Tabbas giya ta Haramta". Zamu taƙaita nan cikin Tafsirin Ƙurɗabi. Amma can gaba, ga mai bincike zai ga inda 'Aliyu bin Abu Ɗaalib ya ce shine aka gabatar domin yiwa ragowar Sahabban da aka gaiyata sallah, har yayi wannan kuskuren. Allahu 'a'alam.

Hadisi daga Littafin Abu Dawud v4 rikici cikin karanta "ƙul ya aiyuhal Kafirun....."

3671. An rubuto daga Aliyu bin Abi Ɗaalib cewar, "Wani Balansare (Mutumin Madina) ya gaiyace shi tare da 'Abdurrahman bin Auf, kuma ya shayar da su giya kafin a haramta shanta (har zuwa lokacin sallar magariba). 'Aliyu ya wuce gaba domin jagorantar sallar magariba, sai ya karanta "Ka ce, Ya Ku Kafirai!..." sai ya rikice (kuskure) cikin karatun surar. Sai wannan ayar ta sauka "Ya Ku Muminai! Kada ku kusanci sallah alhali kuwa kuna cikin maye.....". Hadisi Hasan.

4.5 AYA TA UKU CIKIN HARAMTA KAYAN MAYE:

Allah SWT Ya ce:

إِنَّمَا يُرِيدُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَن يُوقِعَ بَيۡنَكُمُ ٱلۡعَدَٰوَةَ وَٱلۡبَغۡضَآءَ فِي ٱلۡخَمۡرِ وَٱلۡمَيۡسِرِ وَيَصُدَّكُمۡ عَن ذِكۡرِ ٱللَّهِ وَعَنِ ٱلصَّلَوٰةِۖ فَهَلۡ أَنتُم مُّنتَهُونَ

Abin sani kawaĩ Shaiɗan yanã nufin ya aukar da adãwa da ƙeta a tsakãninku, a cikin giya da cãca, kuma ya kange ku daga ambaton Allah, kuma daga sallah. To, shin, ku mãsu hanuwa ne? [Surah Al-Māʾidah: 91]

Wannan itace ƙarshen ayar haramta giya. Bayaninta ƙarara yake babu wani kwane-kwane ko misalai. Ina ga ba sai mun koma ga asbabun nuzul da tafsirinta ba, domin komai ya baiyana kafin ita.

Shine Sahabbai suka ringa fito da tulunan giya suna kwarararwa cikin mugdanan ruwan Madina. Tun daga lokacin Musulmai suka yi bye-bye da giya in banda ɣan kaɗan da Shaiɗan yake fisgar su.

Kamar yadda muka sani ne cewar maganganu da aikin Manzon Allah SAW cikin Sunnar sa su suke daɗa fassara ma'anar ayoyin Alƙur'ani, saboda haka zamu kawo Hadisan Manzon Allah SAW domin daɗa fito da Haramcin shan duk wani kayan maye in Sha Allah.

Akwai Sahihan Hadisai cikin Abu Dawud, Ibnu Maajah, At-Tirmidhi, da sauran littattafan Hadisai inna Manzon Allah SAW ya yi magana dangane da wannan al'amari.

4.6 AHADITH (Hadisai)

Daga littafin Abu Dawud v4 La'ana kan kayan maye da masu ma'amala da su.

An karƁo daga ibn Umar ya ce: Manzon Allah Sallallahu alaihi Wasallama ya ce, "Allah Ya tsinewa giya, da mai shanta, da wanda yake bayar da ita a sha, da mai sayar da ita, da mai sayenta, da mai matsarta (tsuma ta da/ko dafata), da wanda ya sa aka yi ta, da wanda yayi dakwanta, da wanda aka yiwa dakwanta". Sahih.

Daga littafin Bukhari v5 Haramcin kayan maye

4296. An karƁo daga Jabir bin 'Abdullahi cewar ya ji Manzon Allah SAW yana cewa a shekarar buƊe Makkah, lokacin da ya ke cikin garin Makkah, "Allah da Manzonsa sun haramta sayar da giya (watau duk wani abu mai sanya maye).

Daga littafin Bukhari v6 Haramcin kayan maye da kwararar da su.

4620. Anas RA ya ce, "kayan mayen da aka kwararar sunan sa Alfadhikh". Na kasance ina mai baiwa mutane giya a gidan Abu Ɗalha, sai haramcin shan giya ya sauka, kuma Manzon Allah SAW ya umarci wani da ya yi yekuwa ya sanar. Abu Ɗalha ya ce mini "jeka ka jiyo me ake sanarwa?" Na je na jiyo na zo na sanar dasu cewa, "wani mutum ne yake sanar da Haramcin shan giya". Abu Ɗalha ya ce mini "je ka kwararar da ita (ragowar giyar da basu

shanye ba). Sai ga ruwan giya yana gudana kan titunan Madina. A lokacin, sunan giyar da suke sha shine AlFadhikh. Waɗansu jama'a suka ce "Kaɗan daga cikin Musulmai sun mutu a yaƙin Uhud alhali cikkunansu da giya ciki. Sai Allah Ya saukar da S5: A93

لَيۡسَ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ جُنَاحٞ فِيمَا طَعِمُوٓاْ إِذَا مَا ٱتَّقَواْ وَّءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ ثُمَّ ٱتَّقَواْ وَّءَامَنُواْ ثُمَّ ٱتَّقَواْ وَّأَحۡسَنُواْۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ

Bãbu laifi a kan waɗanda suka yi ĩmãni, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, a cikin abin da suka ci (a can baya), idan sun yi taƙawa kuma suka yi ĩmãni, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, sa'an nan suka yi taƙawa kuma suka yi ĩmãni, sa'an nan kuma suka yi taƙawa kuma suka kyautata*. Kuma Allah Yana son mãsu kyautatãwa. [Surah Al-Māʾidah: 93]. Watau abin nufi, giyar da suka sha kafin Haramcinta da kuma bayan Haramcinta da lokaci ƙanƙani, an yafe musu.

Daga littafin Bukhari v3 kwararar da giya cikin hanyoyin Madina.

2464. Anas RA ya ce, na kasance mai raba giya a gidan Abu Ɗalha, kuma a wannan lokacin ana yin giya ne da dabino. Manzon Allah SAW ya umarci wani da ya shelanta Haramcin shan giya. Sai Abu Ɗalha ya umarce Ni da in je in kwararar da ita a kan hanya. Sai na je na kwararar da ita, kuma ta ringa gudu kan titin garin Madina. Wasu mutane suka ce,"An kashe wasu (Musulman) alhali da giya a cikinsu". (A yaƙin Uhud, lokacin Haramcin bai sauka ba). Dalilin

waccan maganar ta Sahabbai sai Allah Ya saukar da "Bãbu laifi a kan waɗanda suka yi ĩmãni, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, a cikin abin da suka ci (a can baya),....."(v.5 :93)

Saboda haka ta'ammali da giya ta kowacce hanya babu fita. Tunda ta kasance Haraamun, to cinikinta harumun ne, haka duk dukiyar da aka tara ta hanyar kasuwancinta HARAMUN ne. Anan ya kamata musan cewar giya na nufin duk wani kayan maye.

Daga littafin Abu Dawud v4 Ta'ammali da kayan maye.

Babi na uku kan Haramcin yin ruwan khal (Vinegar) daga giya.

3675. An hakaito daga Anas bin Malik cewar Abu Ɗalha ya tambayi Manzon Allah SAW bisa wasu yara da a cikin gadonsu akwai giya. Manzon Allah SAW ya ce, "A kwararar da ita". Abu Ɗalha ya ce, "Shin zan iya mayar da ita (giyar) ta koma ruwan Khal?". Annabi ya ce masa "A'a". (Sahih).

Ruwan Khal (vinegar) wani sinadari ne na ruwa, da ake amfani da shi wajen wankewa da tsaftace kayan Gwari da kayan marmari kafin yin amfani da su wajen ci ko dafawa. Sannan ana sirka shi da ruwa a sha domin maganin ƙurajen ciki na cutar ƙyanda ta yara. Haka ana shafawa yara masu fama da ƙyanda a jiki. Wasu ƙabilun na amfani da shi wajen sirka shi da ruwa kwatankwacin yawansa domin ɗigawa jinjirakai a cikin bakinsu da nufin narkar musu da abinda ake cewa yar wuya, wani beli cikin farkon mahaɗar maƙogwaro da baki. Idan ba a sirka shi da ruwa ba, yana da zafi a maƙogwaro kamar

"wisky" sai dai ba ya bugarwa, da kuma wani wari mai zafi a hanci kamar fatar lemon zaƙi. - kenan ba haramun ba ne shansa ko amfani da shi a jiki.

Shima dai ruwan Khal, ana samar da shi ne ta hanyoyi biyu. Ta farko ta hanyar giyar da aka daɗa tsumawa da wasu sinadarin (acetic acid bacteria), wadda wannan hanyar haramun ce. Domin Annabi ya hana ɗaya daga cikin Sahabbansa mayar da ruwan giya ya koma ruwan Khal. Hanya ta biyu ita ce tsuma ɣaɣan itace kafin su kai ga zama giya sai a sanya musu wani sinadarin ko acetic acid bacteria domin ta canza wannan tsimin take ya koma ruwan Khal. Wasu kuma ƙusa suke haɗawa cikin tsimin sai ya koma ruwan Khal ba tare da ya koma giya ba. Wannan hanya ta biyu ita ce ta hallarta yin ruwan Khal, (ma'u khal) a Musulunce.

Mu sani cewar Annabi SAW ya hana tsima duk wani tsimi sama da kwana uku, domin gudun kar ya yi "fermentation" ya koma giya!

Daga Littafin Sunan An-Nasa'i v6.

Babi na 56: Kayan shan da ya halasta a sha da wanda bai halasta ba da yadda ake Yin Ruwan Khal.

5738. An rubuto daga 'Abdullahi bin Ad-Dailami cewa babansa Fairuz ya ce, "Na zowa Manzon Allah SAW Na ce masa, "Ya Manzon Allah, mu mun kasance ma'abota bishiyun inabi (mai tarin

yawa) kuma Allah AWJ Ya haramta giya, saboda haka me ya kamata mu yi da shi? Annabi ya ce, "Ku yi zabib (bushashshen inabi)", sai Na ce, "Me za mu yi da zabib ɗin?" Ya ce, "Ku jiƙa (tsuma) su da safe sai ku sha da yamma. Kuma ku jiƙa (tsuma) su da yamma sai ku sha da safe", sai Na ce, "Ma iya barinsa ya ɗan yi ƙarfi? Ya ce, "Kada ku zuba shi cikin tukwanen kasko, amma ku zuba cikin mazubin fata, domin idan ya daɗe ciki, zai koma RUWAN KHAL (vinegar). Sahih.

Da wannan Hadisi, zamu fahimci halarcin ruwan khal, yin shi da kuma amfani da shi.

Daga Littafin Sunan An-Nasa'i v6.

Duk wani abu mai bugarwa, HARAMUN ne.

5608. An rubuto cewar Ibnu 'Umar ya ce, "Manzon Allah SAW ya yi khuɗuba sai ya karanto ayar da ta yi magana akan "khamr", sai wani mutum ya ce, "Ya Manzon Allah, me za ka ce game da "Mizr" (burkutu)?", Manzon Allah ya ce, "Menene burkutu?", Mutumin ya ce, "Abin sha da ake yi da hatsi a ƙasar Yemen", sai Annabi ya tambaya, "Shin yana bugarwa?", Mutumin ya ce, "E", Annabi ya ce, "Duk abu mai bugarwa, HARAMUN ne". Sahih.

4.7 WASU MASU SON ZUCIYA CIKIN MUSULMAI KO JAHILCI?

Wasu ƙungiyoyin ɓata cikin Musulmai irin Sufaye da Faira sun halastawa kansu shan kayan maye. Kowa yana ganin irin abinda suke yi a kafafen zumunta na sadarwa ta yanar gizo - ɗan Anti da mutanensa. Kodа yake dama waɗannan ƙungiyoyi tuni suka yi hannun riga da Musulunci, ta yadda ƙarara suke yin shirka cikin aiyukansu na ibada. Allah Ya kiyayemu.

4.8 HUKUNCIN WANDA YA SHA KAYAN MAYE

Daga littafin Bukhari v8 Hukuncin wanda ya sha kayan maye.

6777. An karɓo daga Abu Hurairah RA cewar an kawo wani mutum da ya sha giya gaban Manzon Allah SAW, sai ya ce "Ku dakar". Abu Huraira ya ƙara da cewa, "Sai wasu daga cikinmu suka dake shi da hannu, wasu da takalma, wasu da tufafinsu (bayan sun tukuikuye tufan) kamar bulala. Bayan mun gama wasu (daga cikinmu) suka ce masa, "Allah Ya wulaƙanta ka". Jin haka sai Annabi SAW ya ce, "Kada ku faɗa masa haka, domin sai ku taimakawa Shaiɗan ya yi galaba a kansa".

Daga littafin Bukhari v6 Hukuncin wanda ya sha kayan maye.

5001. 'Alƙama ya ce: lokacin da muke cikin garin Hims (a Syria), Ibn Mas'ud sai ya karanta Suratu Yusuf, sai wani mutum ya ce, "Ba haka aka saukar da ita ba". Sai Ibn Mas'ud ya ce, "Na karanta ta haka a gaban Manzon Allah SAW kuma ya tabbatar da haka take, ta hanyar faɗa mini "Da kyau". Ibn Mas'ud sai ya ji warin giya daga bakin wannan mutumin, sai ya ce da shi, "Ba ka jin kunyar faɗar ƙarya dangane da littafin Allah kuma tare da wannan kana cikin giya?" Sai ya yi masa bulala ga haddin da Musulunci ya tanada.

A taƙaice, haddin shan kayan maye, yana ga hannun alƙalin da aka wakkala ya tsayar da shi. Amma yawanci dai bulala ce daga goma zuwa abinda yafi dacewa ga mai shan giyar cikin la'akari da yanayin jikinsa, lafiyarsa da kuma dalilinsa na shan kayan mayen.

Ba wai manufar Musulunci ne a yi ta ɗirkar mutum har ya galabaita don ya sha giya, a'a, ya ishi mutum jin kunya da jin an tozarta shi, ace yau ga shi an kwantar da shi, za a yi masa bulala, koda sau ɗaya za a buge shi, dalilin wani keta haddin Allah da ya yi. Allah ne Mafi sani.

5 KAMMALAWA

Duba ga irin illar da kayan maye suke yiwa mai shansu, ya kamata ɗan Adam ya san cewa Allah Ya ba shi ƙwaƙwalwa kuma Ya fifita shi akan da yawa na daga halittarSa. Duk da Allah Ya baiwa ɗan Adam zaɓi, na yin daidai ko saɓanin haka, to ya kamata mutum ya yiwa kansa ƙiyamul laili ya guji kayan maye ko ba wata aya da ta sauka domin Haramta su. Allah SWT ba abinda da zai ƙaru da shi ko ya cutar da Shi, kabar shan giya ko kar ka bari. Amfanin na komawa ne gareka.

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَوَلَّوۡاْ عَنۡهُ وَأَنتُمۡ تَسۡمَعُونَ

Yã ku waɗanda suka yi ĩmãni! Ku yi ɗã'a ga Allah da ManzonSa, kuma kada ku jũya daga barinsa, alhãli kunã ji. [Surah Al-Anfāl: 20]

TAFSIRIN WANNAN AYA DAGA IMAM QURƊABI

Faɗin Allah Ta'ala "Ya ku waɗanda suka yi Imani! Ku yi ɗã'a ga Allah da ManzonSa.....". Wannan maganar, ga Muminai aka fuskantar waɗanda suka bada gaskiya. An keɓancesu da ita domin girmamawa, banda Munafukai. Allah Ya jaddada musu umarnin yin ɗa'a gareShi da ManzonSa kuma Ya hanesu da juya masa (Annabin) baya. Wannan shine maganar jumhurun al'umma. Kaɗan daga cikin mutane suka ce wannan magana cikin wannan aya, da Munafukai ake kawai. Kuma ma'anarta shine "Ya ku waɗanda suka yi Imani da bakinsu kawai (amma bai kai zuci ba). Ibnu 'Aɗiyata ya ce, kuma wannan zai iya bayuwa ga nesantar da ma'anar saboda

haka (magana ce) mai rauni ƙwarai. Saboda Allah Ta'ala Ya siffanta wanda Yake magana (akansa) cikin wannan aya da Imani. Kuma Imani shine bayar da Gaskiya, shi kuwa Munafiki, ba a siffanta shi da wata Gaskiya ko kaɗan. Haka sun yi nisa (da fahimtar wannan ayar) waɗanda suka ce wai da Banu Israel ake, saboda su Banu Israel a wajen (da'irar) wannan aya (ta Addini na Musulunci) suke.

"Kuma kada ku jũya daga barinsa". Juyawa shine kawar da kai (daga sauraron Manzon Allah da yin aiki da umarninsa). Sai Ya ce "daga barinsa", (shi Annabi shi kaɗai), bai ce daga "barinsu ba", watau (Allah da ManzonSa), domin biyayya ga Annabi, biyayya ce ga Allah. (Barin Annabi, to ka bar Allah ne kwata-kwata. Domin Annabi shi ke kai ka ga Allah SWT).

Shine kamar faɗin Ta'ala "Allah da ManzonSa suka fi cancanta da su (al'umma), su nemi yardarsa", ba a ce "yardarSu ba". Yardarsa - Shi wa? Shi Annabi SAW. Domin idan Annabi ya yarda da kai, to Allah ma Ya yarda da kai. Kuma Annabi ba zai yarda da kai ba, sai kayi abinda zai yarda da kai ɗin a zahiri - shine biyayya gareshi.

"Alhãli kunã ji", wa antum tasma'uuna, mubtadaa da khabar bisa gurbin haal. Watau halin da kuke ciki na jin hujjoji da dalilai (da Annabi SAW yake) karantar da ku daga cikin Alƙur'ani (mai Tsarki).

Ya Allah! Ya Rab! Ya Zal Jalali Wal Ikraam! Ya Wahidul ƙahhaar! Ya Samadul lazi lam yalid wa lam yulad! Muna roƙonKa dacewa

cikin biyayya ga ManzonKa, Muna tuba zuwa gareKa tare da neman GafararKa, cikin abinda Muka gabatar da cikin abinda Muka jinkirtar.

Alhamdu lilLahi wassalatu wassalaamu 'alan Nabiyil Kariim.

Bldr. Ibrahim Muhammad Ɗankyauri. Rajab 1447, Dec. 2025